Food and Agriculture Organization of the United Nations

Global Soil Doctors Programme



Gwajin – Sinadaran Kasa

# TAKIN GARGAJIYA: LURA DA KALA

*Taskar laakari na.10a-10b*

| | | |
|---|---|---|
| MUHIMMANCI | Kalan kasa wani abu ne Mai muhimmanci ta wajen tantance karfin kasa, saboda yana samarda wata hanya ta kaikaice na auna wasu abubuwan da kasa ta kunsa masu amfani wayanda yake ba'a iya ganin su kuma a tantance su cikin sauki, kamar takin gargajiyan dake cikin kasa(OM). Takin gargajiyan kasa yana taka wata muhimmiyar rawa domin dai-daita yanda abubuwa masu rai, sinadarai da kuwa bangalolin kasa ke wanzuwa a cikin kasa, wanda gabadayan su suke tantance lafiyar kasa. A cikin wannan gwajin zamu tantance kalan bangaren kasa na sama ne, idan akwai ishash-shen takin gargajiya, yanayin saman kasan zai kasance mai duhu kuma za'a iya gane iyakan shi idan kalan kasa ya canza yana nuna cangin adadin takin gargajiyan dake cikin kasa dangane da yanda ake amfani da ita ko kuma tattalinta. | |
| KAYAN AIKI |  Dan abin diban kasa | |
| TSARI | 1) Yi amfani da abin diban kasa, a debo sanfurdin kasa a kalla guda biyu: daya a gona, na biyun kuma a cikin wani wuri killatacce wanda ba'ayin komai a wurin |  © S. Pioli |
| | 2) Ayi la'akari da banbance-banbancen kalolin kowane kasa kedashi. Ayi amfani da hotunan dake kasa guda uku na tantan cewa domin gano change-changen da suke acikin kasan. |  © S. Pioli |
| AMFANIN WANNAN HANYAR | Saukin aiwatarwa, babu wani nauran da ake bukata. Yana bada damar gwada kasa daban-daban wayanda suka sami kula daban-daban | |

| | |
|---|---|
| GAZAWAR WANNAN HANYAR | Kala zai iya canzawa, wannan hanyar za'aiya amfani da ita ne kawai akan wata kasa da akasan inda take, wanda yake wasu lokutan yana da wuyan samu. Kala ba a koda yaushe ne yake nufin kai tsaye takin gargajiya ba, kuma ba dukkan kasa ne ke nuna canjin kala ba idan takin gargajiyan kasan ya chanza. |
| TAMBAYOYIN DA ZA'A AMSA | Akwai wasu banbance-banbance kalolin da aka iya la'akarida su daga kasan wararen? Idan akwai banbance-banbance wane kasa tafi baki? Wace kasar kake sa ran tafi takin gargajiya? Wadanne banbance-banbancen ne akayi la'akari dasu a wuraren biyu dangane da ayyukan da akeyi a wurin da kuma yanda shukoki suka rufe saman kasar? Menene kuke tunani yafi samar da takin a wadannan wuraren? Wane abune kukejin zai iya habaka samarda takin gargajiya a wuri/gina? |

| MISALAN GWAJI[2] | | |
|---|---|---|
| MARA KYAU | MATSAKAICIYA | MAI KYAU |
| Kalan kasar yana da haske sasai fiye da na wanda take wurin da aka killace. Baka iya gane inda shinfidan kasar suka rarabe. | Kalar kasar nada haske fiye daba wanda take wurin da aka killace, amma banbancin kalar bai bayyana ba. Kalan saman kasar yana da haske amma ya dan banbanta kadanne da saurar na kasan shi. | Saman kasar yana da duhu kuma akwai banbancin kala sosai da wanda ke binshi. Kalan saman kasar yayi kama da na wurin da aka killace/ Kuma ba'a komai a wurin. |
|  © FAO 2008 |  © FAO 2008 |  © FAO 2008 |

[1] https://www.fao.org/3/i0007e/i0007e00.pdf

[2] As the colour of the topsoil can vary significantly between soil types, the photographs illustrate the degree of colour change rather than the absolute colour of the soil.